| JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA | 24 Rajab, 1443 |
| --- | --- |
| MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI | 25 Febrairu, 2022 |

(1)

## ISRA'I DA MI'IRAJI DA FARLANTA SALLAH

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Ku tsayar da Sallah, ku kuma bayar da Zakka, ku kuma yi ruku'i tare da masu ruku'i)** [al-Baƙra: 43], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai tafiyar Isra'i da Mi'iraji cike take da kyaututtukan Ubangiji, waɗanda Allah mabuwayin Sarki ya keɓance wannan al'umma da su, a cikin manyan waɗannan kyaututtuka akwai sallolin wajibi, wannan babban kyauta ta Ubangiji da take sadar da bayi da Ubangijinsu mai girma da ɗaukaka, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Sai Allah ya farlanta mini salloli hamsin a kowane dare da rana, sai na sauko zuwa wurin Annabi Musa (AlaiHis Salam), sai ya ce: mene Ubangijinka ya farlanta wa al'ummarka? Sai na ce: (Salloli hamsin) sai ya ce: ka koma wurin Ubangijinka ka roƙe shi sauƙi, domin al'ummar ka ba za su iya ba.. haka dai Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya yi ta komawa wurin Ubangijinsa mai girma da ɗaukaka har sai da Ubangiji Mai girma ya ce masa: (Lallai sallolin biyar ne a kowane dare da rana, kowace sallah tana da lada goma, da haka Salloli hamsin kenan).**

Farlanta Sallah a daren Mi'iraji, a kuma saman sama ta bakwai babban dalili ne da yake nuna matsayi da darajar Sallah; lallai sallah kwanciyar hankali ne, da rayuwar zuciya, da kuma abinci mai daɗi ne na ruhi, lallai Sallah Mi'iraji ne na imani, inda mutane suke hawa matakai da suke kusanta su da Ubangijin talikai, Allah mai girma yake cewa: **(Ka yi sujada ka kuma ƙara kusanci da Ubangijinka)** [al- Alaƙ: 19], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Inda bawa ya fi kusa da Ubangijinsa shi ne lokacin da yake sujada),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Ku yawaita yin sujada, domin ba za ka yi sujada ɗaya saboda Allah ba, face Allah ya ɗaukaka darajarka saboda da ita, ya kuma share maka kuskure).**

Haka ma farlanta Sallah a tafiyar Mi'iraji, wani yaye damuwa ne ga Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) bayan ya fuskanci matsaloli masu tsanani a wannan shekarar da aka kira ra da suna (Shekarar baƙin ciki da damuwa); wannan ma wani nuni ne zuwa ga cewa lallai sallah dalili ne na samun natsuwar zukata, da yaye damuwa, da samun kwanciyar hankali, ita Sallah taimako ne na Allah Mai girma da ɗaukaka a lokacin da ake cikin tsanani, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lallai mun san cewa kana damuwa matuƙa da abubuwan da suke faɗi, to ka yi tasbihi ka kuma gode wa Ubangijinka, ka zama cikin masu yin Sallah, ka bauta wa Ubangijinka har zuwa lokacin da mutuwa za ta zo maka)** [al- Hijr: 97- 99], Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Ku nemi taimako ta hanyar yin haƙuri da yin Sallah..)** [al- Baƙra: 45], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(An sanya mini kwanciyar hankali na ne a cikin Sallah)**, (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya kasance yana ce wa Sayyiduna Bilal (Allah ya ƙara

yarda da shi): **(Ya Bilal ka tayar da Sallah, ka sanya mu sami hutu daga cikinta).**

Haka ma a cikin sauƙin da Allah Mai girma da ɗaukaka ya yi na rage adadin Salloli ga al'ummar Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) akwai bayani game da cikan rahamar Allah ga halittarsa; yana kuma nuni zuwa ga sauƙin da Shari'ar Musulunci ta keɓanta da shi, da ɗauke damuwa da wahalhalu, Allah Mai girma yana cewa: **(Allah ba ya ɗaura wa rai komai sai abin da zai iya)** [al- Baƙra: 286], haka ma mai tsarki yana cewa: **(Allah sauƙi yake so maku, ba ya son ku da tsanani)** [al- Baƙra: 185], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai addini sauƙi ne),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah bai aiko don in zama mai tsanani da takura ba, ya aiko ni saboda in zama malami mai sauƙaƙa al'amurra).**

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, shugabanmu Annabi Muhammadu da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Babu shakka kan cewa sallah munajati, da ganawa ne tsakanin mutane da mahaliccinsu mai girma da ɗaukaka, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: Na raba Sallah tsakani na da bawa na zuwa gida biyu, bawa na yana da duk abin da ya tambaya, idan bawa ba ya ce:**

**الحمدلله رب العالمين**

**Sai Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: (Bawa na ya gode mini), idan ya ce:**

**الرحمن الرحيم**

**Sai Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: (bawa na ya yabe ni), idan ya ce:**

**مالك يوم الدين**

**Sai Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: (Bawa na ya yi mini jinjina), idan ya ce:**

**إياك نعبد وإياك نستعين**

**Sai ya ce: (Wannan kam tsakani na da bawa na ne, bawa na kuma yana da abin da ya roƙa, idan ya ce:**

**اهدنا الصراط المستقيم صراط الذين أنعمت عليهم غير المغضوب عليهم ولا الضالين**

**Sai ya ce: (wannan kam na bawa na ne, kuma bawa na yana da abin da ya tambaya).**

Haka ma Sallah tana da tasiri na ban mamaki wajen tsarkake zukata, da gyara rayuwa, da yin ado da kyawawan halaye, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Ka tsayar da Sallah, lallai sallah tana hana aikata alfasha da abin ƙi)** [al- Ankabut: 45], lallai duk mai Sallah na gaskiya ba zai taɓa zama maƙaryaci, ko mai algushi, ko mayaudari, ko maha'inci, ko mai saɓa alƙawari ba, hasali ma zai zama tarin kyawawan ɗabi'u ne da suke kara- kaina a doron ƙasa daidai da manhajin Allah da shari'arsa..

**Ya Allah Ubangiji ka sanya mu da zuriyarmu mu zama masu tsayar da Sallah, ya Ubangiji ka amsa addu'ar mu..**